The Kumbotso Teacher Educator (KUTEJ):
A Journal of Multidisciplinary Studies
Vol 6.1 January 2015 ISSN: 1597-8796

# NAZARIN ALAMOMI DA ISHARORI DA JIKI A MATSAYIN HANYOYIN SADARWA NA HAUSAWA

**Maijidda Ahmad Shuaibu**
Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya Kwalejin Ilimi Ta Sa'adatu Rimi Dake Kumbotso Jihar Kano

**Tsakure**
*Nazarin ishara (wato nuni) wani fanni ne na ilimi wanda ya danganci hanyoyin sadarwa na xan adam amma a wannan takarda za ayi Magana ne a kan isharori gama gari da kyawawan da munanan isharorin Hausa na Hannu kawai an kawo ma'anar Ishara, kuma an kawo ire-iren ishara da ake da su kuma an kawo bayanai na kyawawa da munana koda 'yan yatsu biyu, nuna ido da xanyatsa, tafa hannu gaba, mammatsa hannu , kuma misalan munana tafin hannu, xora hannu aka, yafuce da sauransu. Sannan kuma an kawo ire-iren isharori na duniya da ake da su gaba xaya.*

## 1.0 Gabatarwa

Taken wannan muqala shi ne nazarin alamomi da isharori da jiki a matsayin hanyoyin sadarwa na Hausawa, Al'ummar Hausawa kamar sauran al'ummomi

su ma suna da isharorin nasu na kansu da suke yin amfani da su wajen sadarwa a tsakaninsu. Duk wanda ya kasance ba Bahaushe ba ne babu yadda za'a yi ya fahimci abin da ake nufi sai dai idan ya zauna da Hausawa.

Al'ummar Hausawa sun haxu da Larabawa, kusan a iya cewa haxuwar Hausawa da Larabaawa ta haifar wa da Hausawa Alheri. Domin ta dalilin haxuwar ce suka karbi addinin musulunci, wanda kuma shi ne tsira a duniya da kuma lahira.

Ma'anar ishara kalma ce ta aro wadda Hausawa ke amfani da ita, kalma ce ta Larabci wadda take nufin "nuni" za mu ga Kalmar nuni a wajen Bahaushe su ne ire-iren isharorin da muke da su waxanda suke nuna mana waxansu hanyoyi ne da ake bi ake aika saqonni a cikin al'umma ko nuni ga wani abu ko hani. Misali idan aka ce da mutum /ha/ ana nufin ya bude

Hausawa sun ari abubuwa masu yawa daga larabawa, tun daga yanayin gine-gine da tufafi da abinci, sannan kuma uwa uba harshe, domin kuwa yau harshen Hausa cike yake da kalmomin larabci waxanda ko dai a Hausance su ko kuma suna amfani da su kamar yadda ake aro su daga larabci kamar ishara

Da Hausawa suka ari wannan kalma su ma ba su canza mata suna ba ko ma'ana ba domin kuwa idan aka dubi iren isharorin da Hausawa kanyi don nuni ga wani abu, misali a xauki tagumi. Idan ka ga Bahaushe ya yi tagumi to yana cikin wani hali ne na zulumi ko tunani ko

kuma vacin rai, to haka abin yake ga duk sauran isharorin Hausawa, kowacce da abin da take nunawa.

### 1.1 Hanyoyi Tattara Bayanai

An yi amfani da hanyoyin tattara bayanai da suka haka haxa da tattaunawa da mutane da kuma waiwaye ga wasu ayyuka da suka gabata waxanda suke da alaqa da wannan aiki.

## 2.0 Isharori Gama Gari

Manazarta isharori xan adam sun qiyasta cewa xan adam na yin amfani da isharorin har dubu xari bakwai (700,000) ta yin amfani da fuska da yatsansa da hannunsa da kuma kafaxarsa (Glattan 1981:399). Amma kuma duka kasancewar hakan, sun amince cewa isharori shida ne kawai gama gari. Abin nufi a nan shine wato akwai waxansu yanaye-yanaye, da inka sami kanka cikin a ko ina cikin hausawa za a iya gane abin da yake damunka.

Waxannan yanaye-yaneye kuwa sun haxa da farin ciki da baqin ciki da vacin rai da mamaki da tsoro da qyama da kuma fushi.

Yanzu za a xauki xaya bayan xaya a yi bayanisa dalla-dalla.

i. **Farincin ciki:**(ma’ana ta lugga jin dadi ko mai farin ciki). A ko ina cikin hausawa, idan aka ga baqin ka ya xan xaga sama, kuma ya xan buxe to babu shakka za a gane cewa kana

cikin farin ciki ko kuma kana murmushi to lalle kana cikin farin ciki ne.

**ii.** **Baqin ciki:**(ma’ana ta lugga ta na nufin mai baqin ciki ko mai vacin zuciya ko mai alhini). Idan ko aka bajewar bakinka tare da tashin fatar gira to tabbas za a fahimci cewa haqiqa akwai wani abu da ya vata maka rai, a irin wannan hali da ka sami kanka a cikin mutane za su yi kaffa-kaffa da kai don gudun kada ka huce haushi a kansu.

**iii.** **Mamaki:**(ma’ana ta lugga jin mamaki ko yin farmaki). Idan ko aka ga wangalewar gira da bubbuxewar idanu da kuma washe haqora kaxan, to za a gane cewa lallai wani abu ya ba ka mamaki qwari da gaske.

**iv.** **Tsoro :**( ma’ana ta lugga ita ce jin tsoro, ko fargaba). A ko ina cikin duniya, idan aka ga girarka ta xan xaga sama kaxan tare da xan buxe idanunka kaxan tare da xan buxe baki to babu shakka za a gane cewa kana cikin halin tsoro.

**v.** **Qyama:**(ma’ana ta lugga wani jin si kyama) A ko ina cikin duniya idan aka ga mutum ya xan xaga levensa sama ya doshi rufe qofofin hancinsa, to babu shakka za a fahimci cewa ya kyamaci wani abu ne. Misali mutum ya ci wani abu marar daxi, ko kuma ya ga wani abin kyama wani lokaci ma mutum har yakan saka hannunsa ya rufe hancinsa.

**vi.** **Fushi :**(ma’ana ta lugga ita ce fusata). Idan kuwa aka ga mutum ya xan yi qasa da girarsa tare da rufe idanu kaxan, wani lokaci yana

huhhura hanci ba shakka,wannan fa yana cikin halin fushi.

A taqaice waxannan abubuwa gudu shida da suka gabata su ne isharorin da masana halayyar xan adam suke ganin an yi tarayya da su a duniya.

## 3.0 Ire-iren Isharori

Isharorin Hausawa sun kasu daban daban dangane da yadda ake aiwatar da su. A taqaice za a iya rarraba isharorin Hausawa kamar haka:

1. Isharorin da ake yi da fuska
2. Isharorin da ake yi da hannu
3. Isharorin da ake yi da jiki gaba xaya.

**Isharorin da ake da fuska:** su irin waxannan isharorin sun haxa da irin isharorin da ake yi da ido da baki da ma fuska gaba xaya misali kyifta idanu, da murguxa baki da gyaxa kai da makamantansu.

1- **Isharorin da ake yi da hannu:** Irin waxannan isharorin sun haxa da su kaxa ko girgiza da yatsa ko irin su daquwa ko unbola da sauransu.
2- **Isharorin tsaka-tsaki:** Irin waxannan isharorin sun haxar da irin su kaxa kafaxa da su yanga.

## 3.1 Isharorin Hannu

Qarqashin wannan batu za a duba waxansu daga cikin irin isharorin da Hausawa suke yi da hannu. Su waxannan isharorin na hannu an raba su gida biyu ne, wato kyawawan da kuma munanan isharori na hannu.

## 3.2 Kyawawan Isharori na Hannu

An kira waxannan isharori kyawawa ne saboda ba su da wani abu idan an aikata su domin yin xaya daga aikinsu ba zai Vatawa wani ba. Ko shi wanda ake yiwa ballantana har ta kai ga tashin hankali. Haka kuma shi wanda ya yi ba wai don ya yi ba ne don ransa ya vaci, a a sai dai kawai domin biyan buqatarsa, ko kuma don ya daxaxawa wanda ya yi dan rai (Hassan 1977:9).

## 3.3. Sulluve Hannu

Ana sulluve hannu ne ta yadda mai yi zai tura hannayensa, sai ya xan matse hannun hagun da na dama, ya kuma yi maza ya zare, kamar yadda mai yin alwala kan yi, zai yi wa gabahannayensa haka mafi yawanci zaaji mai sulluve hannu yana cewa uwarta suluf, ubana suluf.

Ma’anar wannan shine mai sulluve hannu yana nuna kuvutarsa ne daga wani abu ko wace, domin wata qila ana so a tsunduma shi cikin wata rigima ko kuma ya mayar da wata amana da aka ba shi, wato kenan nuna ba ruwansa ya fita daga harkar salin alin.

**3.4 Jinjina**(ma’ana ta lugga ya yi wa masu binsa fantankau) anan ana yi wa wanda yayi wani abun kirki ko kokari amma kuma yawan ci amfiwa manyan mutane kamar sarakai da hakimansu a qasar hausa.

Jinjina gaisuwa ce wadda ake yi kamar haka, mutum ya xamqe yatsun hannun damansa, sannan ya miqar da babban xan yatsarsa sama, dominya fuskanci wanda yake yiwa jinjina, amma yanzu kusan wannan

al'ada ta jinjina a qasar Hausa ta xan sami canji, domin kuma a tsaknin samari a kan yi irin wannan gaisuwar, idan wani ya yi abin burgewa, sai ayi masa jinjina.

### 3.5 Tafa Hannu / Sallallami

(Izabella 2007) a wata mukalar ta data gabatar ta ceIdan kaga Baushe ya dora ahannun dama akan na hagu kuma yana tafawa yana cewa la'illaha illallahu Muhammadu-ur-rasullah sall Allahu alayhi wa sallam yana maimaitawa to wani abun al ajabi ne ya faru. m

Idan ka ga Bahaushe yana tafa hannu, to babu shakka wani abun al'ajabi ne ya faru, musamman na rashin jin daxi, ko kuma idan mutum ya manta wani abu ana tafa hannu ne ta buxe hannu. (tafin hannu) biyu a xaga na dama sama a mayar da na hagu qasa, sannan a buga na daman a kan na hagun da xan karfi a wangale baki, a wani lokacin ana haxawa da salati.

### 3.6 Murza/kaxa 'yan yatsu Biyu

Manufar kaxa 'yan yatsu, ita ce a nuna wani abu mai kyau ne, ko kuma mai xaxine, idan abinci ne a kan kaxa 'yan yatsa ne ta hanyar xaukar babban xan yatsa a kan dogon xan yatsa da hanzari za a maimaita sau biyu kofiye da haka.

### 3.7 kallon kasa da sama da nuni dan yatsa

(Izabella 2007 ) a wata mukalar ta data gabatar ta ce Ma'ana ta lugga ita ce kallon kasa da sama da kuma nuna tsana da fushi.

Shi kallon kasa da sama da nuni da xan yatsa a Hausance ya na da manufofi da dama. Zai iya kasancewa wanda ake nunawa xan yatsan da ya zuba ido ka da ya tsoma bakinsa a cikin maganar da ake yi. Yadda ake yi sai a nuna masa yatsun kusa da babban xan yatsa ana nuna masa sai a sauke.

Idan kuwa ka nunawa mutum xan yatsan kuma har ya daxe, ba'a sauke shi ba, to wannan yana nufin mai nuna xan yatsan yana mayar da martani ne na wata maganar da aka gaya masa baiji daxinta ba, kuma za ka ga a irin wannan halin shi mai nuna xan yatsan bai qi a ba hammata iska ba.

**3.8 Jefa Hannu gaba**

Shi jefa hannu gaba a Hausance yana nufin mutum ya xaga hannunsa ya jefa shi gaba, sannan ya yarfar da shi da bayan hannunsa ya jefa shi gaba, sannan ya yarfar dashi na kuma ana yi ne da bayan hannu ba da tafin hannu ba. Idan mutum ya fuskanci wanda ya yiwa ya kuma yi haka da sauri. Lokacin da ake jefa hannun gaba yawanci kai yana xan yin rawa. Ana nufin mutun ya tafi da sauri. Kuma akan haxa da Kalmar tafi ko kuma jeka. Toh a wani lokaci idan aka jefa hannu gaba ya zama zagi. Misali idan aka yi wa mutun zancen wani sai aka ga ya jefa hanun sa gaba yana nufin mutumin banza ne gantali, saboda ya fi karfin ya saurare shi don bai isa komai ba, har akan yi tsaki a irin wannan.

Haka kuma idan mutun ya xan juya tafin hannunsa ya jefa shi gaba, ya yi xan rawa da kansa kuma tave bakinsa to ya ce shi bai san abin ba.

## 3.9 Mammatsa Hannu

Abin da ake nufi da mammatsa hannu shi ne mutum ya riqamammatsa hannunsa ya riqa mammatsa idan wani babba yana masa Magana. Misali, idan mutum yaje wajen sirikinsa bashi da gaskiya to hakan na faruwa, ko wajen shugaban wajen aikinsa ko wani babban mutum da ya ke jin nauyinsa ko kunya, hakkan yana faruwa ne saboda wani dalilai sai a riqa marmatsa 'yan yatsun na jin nauyi ko kunya.

## 3.10 Tafi

Ma'ana ta lugga ita ce tafin hannu

A Hausance ana yin tafi ne, ta yadda mutum zai haxa tafukansa biyu ya rinqa bugawa da qarfiyana bayar da wani sauti fat-fat-fat da sauri.

Kuma ana jin tafi don yabawa ne, ko murna ko farin ciki ko samun nasara a wani al'amari kuma ana yiwa jariri don a yi ma sa wasa da makamantansu.

## 4.0 Munanan Isharori na Hannu

Abinda ake nufi da munanan isharori na hannu, wato waxanda ba su qunshi alheri ba. Waxansu daga cikinsu ma addinin muslunci ya yi hani da su kuma idan an yi sukan jawo tashin hankali ko zubewar mutunci a mutum daga wanin wanda ka yi wa.

Kuma da ma yawanci vacin rai ne yake haddasawa a yi kuma ba a so mutum ya riqa yi sai idan in ya zama dole.

## 4.1 Girgiza Tafin Hannu

Abin da ake nufi da girgiza tafin hannu a Hausa shi ne, mutum zai ware tafin hannunsa na dama ya girgiza da sauri, tare da an tave baki da kuma sunkuyar da kai kaxan sai mutum ya dubi wanda yake so ya ba wa labarin wani lokacin akan girgiza hannu a gaban mutum idan da wasa a tsakaninsu.

To, a duk lokacin da Bahaushe ya yi hakan to yana gayawa wannan mutum mai kallon nasa xin cewa mutumin a shashasha ne. Wato ana nufin bashi da cikakken hankali, ya san irin yadda zai yi harka da shi. Marasa hankali kawai ake yiwa kuma ba a idon mutum ba idan kuwa ya gani idan mahaukaci ne to sai yadda ta kasance.

## 4.2 Nuni da Xan Yatsa

Nuni da xan yatsa a Hausance shi ne mutum ya yi nuni da dogo yatsansaya nuna mutumin dayake yiwa ya gani sosai ana karkaxa shi daga nuni da xan yatsa sai kuma a zarce da lakuce hanci idan ya girma ma wato ya zama hatsaniya.

Idan mutum ya nuna kaxa xan yatsa yana nufin raini ne ga mutum, vacin rai yake kawo nuni xan yatsa, hakan yakan sa tashin hankali.

Kuma hausawa basa son a nuna su da xan yatsa. Idan kuma ya xaga xan yatsa, yana jin kashedi lokacin da ake yin nuni, ko kuma ka kiyaye ni, ko ko fita hanyata, ko kayi hankali da kanka ko kanki da sauransu.

### 4.3 Umbola/Dakuwa

A Hausance idan mutum zai yi umbola/dakuwa to zai buxe 'yan yatsunsa biyar, ya daidaici wanda yake yiwa da su.

Idan mutum ya yi umbola ana nufin zagin uwa, ance wa wanda aka yiwa (uwarsa) ke nan. Idan kuwa a saya sai a ce gidanku ko a ce ka ci gidanku, ana yin umbola tare da giirgiza hannun wato tare da kashedi kuma manya ne ke yi wa yara, kuma ana yiwa babban da aka raina.

### 4.5 Yafuce

Shi wannan abu da hannu ake yinsa mutum zai buxa hannunsa ya yi sama da 'yan yatsunsa na gaba xaya sannan kuma ba a yafuce ko wajen kiran babba ko yara.

Shi dai yafuce kira ne, wanda ake nuna kalmar 'zo' ko kuma a ce 'yaka nan'.

### 4.6 Dunqule Hannu

Dunqule hannu zagi ne mai ciwo kamar yadda umbola take zagin uwa shi dunqunle hannu zagin uba ne (wato an ce da mutum ubansa kenan).

Yadda ake dunqule hannu shi ne mai yi sai ya damqe gaba xayan ‘yan yatsunsa kamar dai yadda mai jinjina yake yi sai ya nuna mutumin da ake nufi ya daidaice shi sosai. Lokacin da mutum yake yi za a ga fuskar mutum a vace, bambancin dunqule hannu da jinjina xaya ne kawai wajen miqe babban xan yatsa a dunqule hannu to a wajen dunqule hannu miqe shi ake yi a kamar wajen jinjina.

## 4.7 Xora Hannu A ka

Xora hannu a ka yana nufin baqin ciki ko takaici ko cuta. Idan mutum wani abu ya dame shi to yakan xora hannu aka ya yi kuka ko ihu. Misali idan mutun ya rasu , a kan xora hannu a ka ace ‘wayyo Allah na shiga uku’ to alamar wata damuwa ko cuta idan mutum azaba tayi masa yawa sai ya xora hannu a kan sa ya zabura yana kuka.

## Kammalawa

Wannan muqala an gabatar da ma’anar da isharori da ire-iren da kuma isharori gama gari da kuma kyawawa da munana isharorin Hausawa, daga farko an yi bayanin isharori gama gari farin ciki, bakin ciki, tsoro, mamaki, fushi, sannan kuma aka yi takaitaccen bayani akan ire iren isharorin Hausawa da ake yi da fuska, da hannu da kuma jiki gaba daya.daga karshe kuma aka yi bayanin kyawawa isharori kamar haka sullube hannu, jinjina, tafa hannu, murza/kada ‘yan yatsu biyu, nuna ido da dan yatsa, jefa hannu gaba, mammatsa hannu, tafi, sannan aka yi bayanin munanan isharori na hannu kamar

Girgiza tafin Hannu, nuni da dan yatsa, umbola/dakuwa, yafuce, dunkule hannu, dora hannu a ka.

Haka kuma idan aka dauki wannan ishara suna da yawa shiyasa aka dauki wani bangare aka yi Magana da yawa kuma wasu masu nazarin ma za su ci gaba da bincike ta wani bangaren.

**Manazarta**


*Growther, J (1998) Oxfoerd Advanced Learners Dictionary English. Fifth edition, England, Oxford University Press.*

*Glattan, A.A (1981) the English Book A Complete Course USA Science Research Associate Inc.*

Gumel, M. A (1996) Hanyoyin Sadarwa na Gargajiya: Sigoginsa da Muhimmancinsa ga rayuwa Hausawa. Kudnin Dirgiri na fako Jami'ar Bayero

Yahaya, I.Y (1998) Hausa a Rubuce Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa Zaria, Gaskiya Corporation.

Yule, G. (1996) The Study of Language 2nd Edition United Kingdom Combridge University Press.

Adamu, N. (1995) Isharorin Hausawa da yadda Mata ke Gudanar da su da Muhimmancinsu a Tsakanin Al'ummar Hausawa.

Hassan, M.B (1977) Kuraya ma Jawabi na Sashen Harsunan Nijeria, Jami'ar Bayero Kano.

Saddik, A.Y (1994) Hanyoyin sadarwa na Yara Qanan, Kundin Digirin Farko Jami'ar Bayero Kano.

Maijidda A. S. (2006) Nazarin isharorin Hausawa Post Graduate Diploma in Hausa, Jami'ar Bayero Sashen koyar da Harsunan Nijeriya, Kano.

*Kamus Na Turanci Da Hausa (2007) 10th edition the Northern Nigerian Publishng Company Ltd*

Izabella Will (2007) Gestures and indirect statement as means of expressing emotions and opinions among Hausa women, University of Warsaw.